# Ku sauƙaƙa kada ku tsananta, ku yi bushara kada ku yi kora

Daga Anas Ɗan Malik Allah Ya yarda da shi, daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: Ku sauƙaƙa kada ku tsananta, ku yi bushara kada ku yi kora.
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana ba da umarnin sauƙaƙawa da rangwame wa mutane, da kada a tsananta musu a dukkanin lamura na addini da na rayuwa, wannan kuwa a daidai yadda Allah Ya halatta Ya kuma shar'anta. Kuma yana kwaɗaitarwa a kan bushara da alheri, da rashin korar (kyarar) mutane.

https://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/5866